# Haƙiƙa ka yi tambaya game da wani abu mai girma, kuma cewa shi mai sauƙi ne ga wanda Allah Ya sawwaƙa masa

Daga Mu'az ibnu Jabal - Allah Ya yarda da shi - ya ce: Na ce: Ya Manzon Allah! Bani labarin aikin da zai shigar da ni aljanna kuma ya nisantar da ni daga wuta, ya ce: «Haƙiƙa ka yi tambaya game da wani abu mai girma, kuma cewa shi mai sauƙi ne ga wanda Allah Ya sawwaƙa masa ka bautawa Allah kada ka hada shi da kowa, ka tsaida sallah, ka bada zakka, ka azumci Ramadan, ka ziyarci Ɗakin (Allah). Sannan ya ce: Shin ba zan shiryar da kai zuwa ga ƙofofin alheri ba? Azumi garkuwa ne, sadaka tana shafe zunubi kamar yadda ruwa yake kashe wuta, da kuma sallar mutum a tsakiyar dare, sannan ya karanta: {Sasanninsu suna nisantar makwanci} har ya kai (suna aikatawa). sannan ya ce: Shin bana baka labari da asalin al'amari ba da ginshiƙinsa da kuma ƙololuwar tozansa, sai na ce: Na'am ya Manzon Allah, ya ce: Asalin al'amari shi ne Musulunci, ginshiƙinsa ita ce sallah, kuma ƙololuwar tozansa shi ne jihadi. Sannan ya ce: Shin bana baka labari ba da abinda zai haɗa haka gaba ɗaya ba? na ce: Na'am ya Manzon Allah! Sai ya riƙe harshensa kuma ya ce: Ka riƙe wannan, na ce: Ya Annabin Allah! Muma za’a kama mu da abin da muke magana da shi? sai ya ce: Babarka ta yi wabinka ! ai ba wani abu ne yake afkar da mutane ta fuskokinsu ko ta hancinsu ba sai abin da harsunansu suke girba».
[Ingantacce ne] [Tirmizi ne ya ruwaito shi]

Mu'az - Allah Ya yarda da shi - ya ce: Na kasance tare da Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - a wata tafiya, sai na wayi gari wata rana a kusa da shi alhali mu muna kan tafiya, sai na ce: Ya Manzon Allah ka bani labarin aikin da zai shigar da ni aljanna kuma ya nisantar dani daga wuta, Ya ce: Haƙiƙa ka tambayeni daga wani aiki mai girman aikatawa ga rayuka, kuma mai sauƙi ne ga wanda Allah Ya sawwaƙa masa; ka yi farillan Musulunci: Na farko: Ka bauta wa Allah Shi kaɗai kada ka taranya wani abu da Shi. Na biyu: Ka tsaida salloli biyar na farilla a yini da dare: Asuba, da Azahar, da La'asar, da Magariba, da Isshai, da sharuɗɗansu da rukunansu da wajibansu. Na uku: Ka fitar da zakkar farilla, ita ce ibada ta dukiya wajiba a kowace dukiyar da takai wani gwargwado abin iyakancewa a shari'a, ana bada ita ga waɗanda suka cancanceta. Na huɗu: Ka azimci Ramadan, shi ne kamewa daga ci da sha da wasunsu daga abubuwan da suke karya azimi da niyyar bauta, daga ɓollowar alfijir zuwa faɗuwar rana. Na biyar: Ka ziyarci Ɗakin Allah, da nufin Makka dan yin ibadun aikin Hajji, dan bauta ga Allah - Mai girma da ɗaukaka -. Sannan tsira da amincin Allah su tabbata agare shi ya ce: Shin ba na sanar da kai hanya mai kaiwa ga ƙofofn alheri ba? hakan da bin waɗancan farillan da nafilfilin: Na farko: Azimin nafila, shi mai hanawa ne daga afkawa cikin

saɓo, hakan da karya sha'awa, da kuma rage ƙarfi. Na biyu: Sadakar nafila tana kashe laifuka bayan an aikata su kuma tana tafiyar da su tana kuma shafe su. Na uku: Sallar dare a kashi ɗaya bisa uku na ƙarshen dare, sannan tsira da amincin Allah su tabbata agare shi ya karanta faɗinSa - Maɗaukakin sarki -: {Sasanninsu suna nisanta} wato: Suna nisanta {Daga makwantansu} wato: Wuraren kwana { Suna kiran Ubangijinsu} da yin sallah da zikiri da karatu da addu'a, {Dan tsoro da kwaɗayi kuma suna ciyarwa daga abinda muka azirta su, wata rai bata sanin abinda aka ɓoye musu na abinda ido yake farin ciki da shi} wato abinda idanunsu zasu yi farin ciki da shi a ranar Alƙiyama da kuma aljanna ta ni'ima, {Dan sakamako da abinda suka kasance suna aikatawa}. Sannan tsira da amincin Allah su tabbata agare shi ya ce: Shin bana baka labari da asalin Addini ba? da ginshiƙinsa wanda yake dogaro akansa? da ƙololuwar tozansa? Mu'az - Allah Ya yarda ad shi - ya ce: Eh, ya Manzon Allah. Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - ya ce: Asalin al'amari: Musulunci shi ne shaidawa biyu, kuma dasu ne tushen Addini zai wayi gari tare da mutum. Ginshiƙinsa: Sallah, babu Musulunci ba tare da sallah ba, kamar yadda babu gida ba tare da ginshiƙi ba, wanda ya yi sallah Addininsa zai ƙarfafa zai ɗaga; kuma ƙololuwar tozansa da ɗaukakarsa yana kasancewa ne da yin yaƙi da yin ƙoƙari a yaƙar maƙiya Addini dan ɗaukaka kalmar Allah. Sannan tsira da amincin Allah su tabbata agare shi ya ce: Shin ba na baka labari da kyautata abinda ya gabata ba? sai - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - ya riƙe harshensa, ya ce: Ka hana wannan kada ka yi magana da abinda bai shafeka ba. Mu'az ya ce: Shin Ubangijinmu zai kamamu Ya yi mana hisabi da dukkan abinda muke magana da shi?! Tsira da amincin Allah su tabbata agare shi ya ce: Mahaifiyarka ta yi wabinka! ba ana nufin mummunar addu'a akansa ba, sai dai yana daga zancen larabawa dan faɗakar da shi zuwa wani al'amarin da ya kasance yana kamata ya farka da shi ya kuma san shi, sannan ya ce: Ai babu abinda yake afka mutane ya jefasu cikin wuta ta fuskokinsu sai abinda harasansu suke girba na kafirci da ƙazafi da zagi da yi da mutum da annamimanci da ƙagen ƙarya da makamancinsu.

https://sunnah.global/hadeeth/ha/show/66530